Kai tsaye ta murda kofar dakin ta shige tana qaramar sallama da cewa"

Umma yaganah yauma bazan fita koinaba fuskana ta sake kumbura da ja...

Zaune umman take kan wata tattausar sofa kalar ash na komai dakin dayake ash Mai haske,

Farin glass ne a idonta tana karanta wani Arabic hisnul Muslim
Jikinta sanyeda doguwar rigar plain cotton Swiss Mai tsada light pink.

Dagowa tayi tana kallon Inayah cikin kulawa da tsananin bayyananniyar kaunar Inayah data Dade da shiga jininta ta ajiye littafin gefe kan table tareda maida hankalinta kan Inayan gaba daya tace"

Yau kam saikin fita Inayah,
Meyesa kike Wasa da karatunki ne yanzu?
So kike abbinki ya dawo yasan kwana biyu bakya zuwa makaranta?
Karatun likitanci fa kikeyi karki manta,
Ahakan zakiyi wani abin arziki kullum cikin shiriritar Gayu ya hanaki Wannan da wancan?

Akan pimples bazakice kindaina fitaba sai kin warke Dan haka
Ki Gama breakfast kije kiyi Shirin zuwa makaranta.

Zama Inayah tayi gefen umman tareda yamutsa fuska tana kokarin yin magana umman ta katseta tana cewa"

Abbinki kinfi kowa sanin fadan bacin ran dazai nuna Idan yasan kina skipping ranakun zuwa school,
Banason bacin ransa akan Rashin dalilinki.

Kai Umma yaganah Abbi fa idan yaji abinda ya hanani zuwa bazaiyi fada ba.

Inayah please Mana,
Ki daure ki cire Rashin son makaranta a ranki bayan kinsan Abbinki yanada riqaqqen raayi akan son karatunki.

Bari sai Akira likita tazo ta sake duba fuskar taki,ok?

Gyada Kai tayi tareda miqewa tana kokarin barin dakin tace"

Good morning,ban gaishekiba Dana shigo.

Wani qayataccen murmushi Umma yaganah ta sake tana kallon fatar wuyan Inayar dake bayyane tana sheqi sbd yanayin rigarta cikin Yar dariya tace"

Barkanki da safiya kema Inayah Majeed.

waiwayowa tayi ta kalli Umman tana Yar murmushi sbd friends dinta ne masu Kiranta Kai tsaye hakan Amma ko umman sau tari hakan take kiranta itama.

Dining ta nufa ta zauna hankali kwance Tasha black tea da toasted bread biyu da kwai ta tashi tabar gurin ta nufi dakinta tana sake Danna Kiran Mahaifinta dataketa Kira tun dazu takasa samunsa sai yanzu Kiran yashiga.

***Zaune yake a palon madaidaicin duplex dinsa dake Singapore tareda CM Nuradden Aminin huldodinsa suna meeting akan aikin da zaaiwa sabon kamfaninsa da aka bude reshensa a portharcourt Nigeria.

Kan couch Mai zaman mutum biyu yake zaune sanyeda sky blue English kaftans masu tsananin taushi da tsadar dake bayyane.

Wayarsa dake gefensa ajiye ya waiwaya a natse ya kalla ganin hasken data kawo alamar shigowar Kira ko saqo.,
Fararen idanuwansa yafara Dan juyowa ya kalla CM Nuradden dasu Ahankali cikin nutsuwa yace"

One minute.

Hannunsa yakai ya dauki wayar kai tsaye tareda kaiwa kunnensa cikin nutsuwar murya da Allah yayi masa Mai tattareda kamewa saidai kasancewar 'yarsa ce tilo datafi masa kowa da komai daya mallaka a duniya ahakan muryar tasa a bayyane take da kauna da kulawa
Kai tsaye ya furta"

Yes,INAYAH.

wata ajiyar zuciya ta sake tana zama bakin gadon dakinta cikin tsananin kauna da kewan mahaifin nata tace"

Good morning Abbi.

Ahankali ya dago fararen idanuwansa ya kalli agogon _Patek Philippe_ dake daure a hannunsu ya maida idanuwanta ya dan kalli CM Nuradden
yasan Inayah zataci lokacin magana dashi sosai Dan Kuma CM flight zaibi yakoma Nigeria zuwa 11 dan haka Kai tsaye cikin nutsuwa da kulawa yace"

Morning Inayah,
Kintashi Ify?

Lfy kalau,
Abbi haryanzu kana Singapore?
Yaya aiki?
When are you coming back?

Cikin nutsuwa ya amsa ta da cewa"

Inayah Ina magana da CM yanzu,
Anjima I will you back,ok?
Ki kula,Ki gaida Umma yaganah.

Ok Abbi sai anjima.
I miss you.

Kashe wayar yayi tareda ajewa gefensa kafin ya dago ya kalli CM dake jiransa dan harya fara shiga yanayi na damuwa sbd sanin wayar Inayah ga mahaifin nata sai tasa a rasa meetings masu mahimmanci dazasu kawo manyan dukiya da dama Dan ansaba
Indai akan Inayah ne AA MAJEED nada raunin duba al'amura da dama masu mahimmanci Kuma hakn wani al'amarine da kusan duk wnada yake hulda ko mu'amala dashi yasani,

'yarsa Inayah itace Rauninsa da kowa yakasa sani duniya akansa sai Aminin nasa Cm Nuradden sai Kuma Umma yaganah sbd sune sukeda cikakkiyar shaidar yanda 'yarsa take a Ransa fiyeda duk abinda yakeda,

Hakama 'yarsa Inayar itace qarfin Rayuwarsa,
Duk Wannan arzikin da dukiya Mai yawan daya Tara basukai masa mahimmancin farin cikin yarsa na wuni daya ba,

Inayah da kanta tasan itace hasken rayuwar Mahaifinta kaman yanda itama kowa yasanta yasan Mahaifinta shine abinda Bata iya hada girma da tsananin kaunarsa da komai,
Shine Abbinta,shine mahaifi Uba Kuma mahaifi UWA.

Numfashi CM ya sauke ya sauke yana kallon A MAJEED din sbd ya dauka zaman jiran yagama wayar ya samesa ne saigashi Allah yasa yau A MAJEED din ya taqaita.

A MAJEED ya fahimci zullumin da CM ya shiga dan haka ya taqaita wayar
Cikin nutsuwa ya dauki takardun da zai saka hannu akai yafara signing Yana cewa"

Sauran takardun na AIA sa hannun Inayah zaa saka a takardun Amma ba yanzuba saita kammala karatunta tukuna so agama aikin kawai kafin lokacin.

Alright Inshallah.

Sai 10 suka rabu da CM bayan daya daga cikin ma'aikatansu yakaisa airport ya wuce.

11:30 shima yabi jirgi tareda secretary dinsa suka bar Singapore zuwa Australia.

****Badan tasoba haka tayi Shirin makaranta ta fice daga gidan zuwa school bayan tayi waya da qawarta da itama duk sunne ba wani son karatun sukeba sunfi ganewa Gayu da rayuwa kawai irin ta 'yayan gata masu abin duniya.

Duk da Bata wani son karatun sosai bashi yasaka Bata maida hankali ga karatunba idan taje, Wuyarta dama dai taje din sbd idan taje sosai take maida hankali ga karatun Kuma Allah ya taimaketa tanada qwaqwalwar daukan karatun sosai Dan ahakan Bata taba failing ba Koyaushe tana samun grades masu kyau,
Kawai dai Allah Bai saka Mata wani son karatun bane
Abinda Allah yasaka Mata so shine Tanada shaawar yin aure kawai sbd ta daina zuwa makaranta tayi rayuwarta yanda taga dama daga shopping sai zuwa beauty parlor dasu spa sai yawan qasashen dataga dama.,

Ko yanzu kusan rayuwarta hakanne,
Batada wani aikin bayan yawon shoppings da zuwa su spa day guraren gyaran jiki sbd Bata hada gyaran jikinta da komaiba Wanda kusan hakanne yasa koyaushe fatarta da jikinta koina yake sheqin hutu da lafiya cikakkiya da zallar gyara na musamman,

Yawon qasashene Bata wani Yi sbd duk qasashen datake zuwa tareda Abbin take zuwa kokuma zuwa umrah ko Hajj tareda Umma yaganah Dan haka Bata wani samu tana yawon yanda takeso sbd haryanzu dasuka samu sauyin rayuwa mai tsananin nisa Abbinta baya barinta tana yawo yanda takeso duk da kuwa ba wani zama yakeyiba Amma dokarsa na aiki a gidan duk inda yake kuwa.

Hakan yasa takeson aure fiyeda karatu musamman ma auren irin na wayayye irinta dazai barta tayi rayuwar datakeso ta Rashin takura da damuwa kawai suyita soyayya suna shaqatawa sbd love na cikin abubuwan datake yiwa kanta shaawar samun kanta aciki hakanne ma yasa bayan abbinta da yaganah to Babu Wanda takeso sama da saurayinta Zaid.

Soyayyar Zaid tayi wani irin nisa a ranta Kaman yanda shima yake tsananin son Inayan,

Kusan yanayin rayuwarsu daya sbd shima iyayensa masu arzikine sosai Amma suna Nigeria Dan asalin portharcourt ne karatu yake a qasar,
Kaman yanda take wayayyar Yar gata girman turai hakan yake shima sbd tun Yana yaro shima kusan a qasahen turawan ya tashi tareda iyayensa sai daga baya Suka koma gida sukabarsa Yana karatu.

Dan haka da rayuwar Zaid tayi daidai da tata sai soyayyarsu takeda wani irin qarfi da shaquwa.

Abbinta yasan raayinta na Rashin maida hankali kan karatu yakuma san aurene takeso fiyeda karatun Amma yaqi nuna Mata ya sanin sbd karta sake samun damar nuna batason karatun, Shikuma raayinsane riqaqqe dakuma buri akan bazatai mata aureba saita Gama karatun.
##MAMUH#
#ZAFAFABIYAR#
#AA MAJEED#
#AYSHATOUH INAYAH#
#LOVE
#ROMANCE
#MARRIAGE

_ZAFAFA BIYAR_

*_INAYAH_*
_MamuhGee_

*_GURBIN IDO_*
_Safiya Huguma_

*_SANADIN LABARINA_*
_Hafsat Rano_

*_FARHATAL QALB_*
_(Miss Xoxo)_

*_BABU SO_*
_Billyn Abdul_

_*Littafi daya 300*_
*_Littafi biyu 400_*
*_Littafi uku 500_*
*_Littafi hudu 700_*
*_Littafi biyar 1k_*

_BREAKDOWN OF ZAFAFA BIYAR VVIP SINGLE PAID BOOK_

_4 BOOKS  4500_
_3 BOOKS : 3500_
_2 BOOKS : 2500_
_1 BOOK: 1500_

YADDA ZAKU BIYA KUDIN BOOKS👇🏾👇🏾👇🏾

ZENITH BANK
HAFSAT UMAR KABIR
2270637070

SEKU TURA SHEDAR BIYA TA:
07040727902

IDAN KUMA KATI NE SEKU TURAWA👇
09134848107
[9/30, 1:58 PM] MG: *_Mamuhgee 10_*
*_Arewabooks@Mamuhgee_*
Karfe uku na yamma ta dawo daga makaranta tareda qawarta neesah wadda kusan ra'ayoyi da halayensu suke duk iri daya,

Neesah Bata kaunar karatu kusan fiyeda Inayah ma Kuma itama tanada qwaqwalwar daukan karatun Amma tamafi nisa Rashin maida hankali kan karatun sbd ita iyayenta basa takura Mata ko Bata wata doka da Oda duk kuwa da kasancewarsu musulmai Kuma hausawa kamansu Inayah,

Iyayenta ita har tafiye tafiyen wasu guraren suna barinta Amma qawancenta da Inayah yasa Bata tafiyar koina itama sbd tare suke komai to Inayah Kuma abbinta baya Wasa Sam Sam bare sake fuska ga irin Wannan shashancin Duk da kuwa ko ita neesar tana fada son da iyayenta ke Mata itada takeda uwa da uba wasane akan Wanda Abbin Inayah yakewa Yar tasa Amma duk da Wannan tsananin kaunar A.A MAJEED bai taba bada fuska ko daga qafaba akan tarbiyar 'yarsa,

Kaman yanda yake tsayayye akan dukkanin huldodinsa magana daya yakeyi baya sauyi to kusan hakanne akan Inayah,
Dokarsa tun tana qanqanuwa haryanzu Bata daina aikiba sbd a gurinsa har yau har gobe Inayah jinjira ce agabansa.

Taren Inayah da neesah yasa akan Dole itama neesah din yau da gobe Ahankali ta sauya bangarori da dama dan tana samun tarbiyar Inayah na shafarta sbd dukkanin kiyayewa da dokokin Abbin akan Dole itama ta koya binsu tunda Inayah Bata tsallakesu Dan haka itama tunda tana kaunar Qawar tata Dole ta ringa bin tarbiyar,

Ahakan sai rayuwarta taqara Mata Dadi sbd Ashe tarbiyar da tsawatarwar tanada Dadi sosai musamman Idan Umma yaganah ta zauna tana musu fadan wani abin idan sunyi sai su gyara ko basa so ahakan sai suga ba illa bane kuwa gyaran.,

Ko sallah da bawani sosai neesah takeyiba sbd Rashin ilimin addini da tarbiya sosai duk sanadin tarenta da Inayah yanzu babu sallar datake tsallakewa saidai wata ayita ba acikin lokaciba Amma komai dare idan batayiba saita rankasu take kwanciya.

Bangaren saka sitira ne dai haryanzu sai ahankali bawani sitirar Daya kamata take sakawaba shima sbd itama Inayan tana saka qananun kayan sosai ne sai Suka hade Amma Kuma ita Inayah wasu lokutan tamafi saka dogayen riguna irinsu Turkish ko Kuwait abayas fiyeda qananun kayan.

Iyayen neesah kuwa Suma Dadi suka ringa ji sosai ba kunya har Kiran Umma yaganah suke suna godiya akan tarbiyar dasu Suka kasa bawa yarsu suna son Kiran Abbin Inayah amma AA MAJEED ba gurinda zasuyiwa dogon shishigi bane bare shima su ringa Kiran suna godiya Amma a hakan dai dad din neesah Bai daina cusa kansaba sbd dama dalilin dazai hada hulda da A MAJEED din yake nema tuni.

Tare Suka jero kai tsaye suna shigowa cikin yalwataccen palon dake farko na cikin babban gidan nasu,

Inayah sanye take cikin free Malaysian Abaya ash kala da Adon black beads sai black silky scarf dayake kanta daure hasken fatarta ya fito sosai sbd black kalar dake jikinta,
Neesah Kuma Kaman dai yanda kusan aka saba turtle neck Balenciaga top ce a jikinta brown da Alvn straight skirt shima brown.

Zubbi ce data fito daga hanyar kitchen daukeda tray da drink akai da cup ta nufi inda zata ajiye ta aje ta qaraso gurinsu cikin girmamawa da sakewa ta karba handbag din Fendi dake hannun Inayah tana cewa"

Sannu da dawowa Inayah.

Kallon neesah tayi tana cewa"

Welcome Ms Neesah.

Thank you" Suka furta Mata kusan state suna qarasowa tsakiyar palon.

A hankali idanuwan Inayah Suka sauka kan kyakkawar fuskar dake zaune palon ta Dr Farhat Ahmed
Kwararriyar likitar Mata dake amatsayin likitarsu wadda itace ta saka kanta hakan sbd tsananin

kaunar A MAJEED dake dawainiya da rayuwarta,
Taqi aure har shekarunta sunja sosai sbd qwallafa ranta datayi akan Abbin Inayah shikuma duk dubaru da dadin Baki da komai da Inayah da Umma yaganah sukeyi Akan ya aura Dr Farhat din Sam babu haske qarshema sosai sukaga bacin ransa akan hakan daga lokacin Basu sake Shiga hurumin maganar yayi aurenba,

Inayah da Umma yaganah sunsan cewa bazai taba aureba sai Lokacinda ya aurar da Inayah Wannan Kaman wani raayine nasa wanda yaketa damun Umma da Inayah din sakamakon hakanne shaawar yin aure tashiga Inayah sosai sbd tayi aure da wuri kodan sbd Abbinta yayi aure tunda bazaiyiba sai ya aurar da ita din.

Wannan sanadin ne yasa takeda buri da kaunar aure batareda ta tsaya dogon karatu ba, Saigashi raayinta ya kama qawarta itama aure takeson yi ba karatunba,

Dr Farhat tun kafin Bayyanar A MAJEED da 'yarsa rayuwarta batada wani Mai nemanta da aure ga shekarunta sun Dan fara ja Dan haka tana ganinsa taji Aurensa shine qarshen abinda takeso a duniya dan haka ba Wasa ta maqale tanata fama da wahalarta ita kadai Amma yanda Inayah ta shaqu da ita tayi Mata alqawarin tsaya Mata sai abbinta ya aureta.

Cikin sakewar fuska da farin cikin ganinta Inayah yaqaraso tana cewa"

Yanzu kika zo ko tintini Dr Farhat?

Miqewa tsaye Dr Farhat tayi tana Dan rumgume Inayan tana cewa"

Just 3 min kenan da shigowana,

Ok,sannu da zuwa,
Umma yaganah Bata Nan ne?

Zama sukayi cikin nuna damuwa Dr Farhat ke kallon fuskar Inayah tana cewa"

Umma takirani kina fama da Rashin lafiya a fuska
Hankalina yatashi so I had to come
Banma dauka kin fita school ba.

Dan kwabe fuska tayi tana cewa,

"Nafita Amma gaskia dama Ina buqatan ganin likita.

Ba wani sauran Bata lokaci suka miqe suka dunguma zuwa gurin umma yaganah suka sanar mata zasu asibiti.

Ficewa sukai a motar Dr farhat din suka nufa asibiti gurin likitan fatar dashine zai duba Inayah din.

Sai yamma sosai suka dawo gida ta ajeta ta wuceda Neesah ta kaita gida itama.

Dakinta ta wuce direct ta tube tayi wanka tareda alwala tayi sallar magrib
Tana idarwa taga time din ishai yayi dan haka ta miqe ta yi sallar tana gamawa tayi adhkar tagama ta miqe ta sanya riga da wando na bacci masu Dan kauri da safa sai hular dake hade da rigar sanjin jikinta data rufawa kanta ta zira slippers din Gucci.

Fitowa tayi daga dakinta Tana amsa wayar zaid cikin wani irin yanayi sanyin jiki da sakewa dakuma taushin murya kaman yanda tasaba waya dashi saidai Kuma sanyin jikin na rashin ganin Abbi ne gabaki daya tunda yayi tafiya ya dawo.,

Hanyar dazata kaita palon abbin ta nufa Kai tsaye Tana cigaba da wayar hankalinta na Dan rabuwa biyu sbd kaman yanda abbinta baya hada komai da 'yarsa itama kam tamafi sa Dan kuwa ita batamasan komai da kowaba dake gaban mahaifinta tunda shi kadai ta taso da sani.

Abbin yasan da soyayyarta da Zaid duk da irin tsananin dokokin dake gidan gameda tarbiyarta Amma Sam Bata tsaya nuqu nuqu ko Bata lokaciba ta fada Masa Zaid din Dan tasaba Bata iya boyewa mahaifinta komai Kuma kusanma shine yabata tarbiyar hakan yayi mata sabo sosai da rashin boye Masa komai sai tsananin gata da wayayyar rayuwar turai dasuke ciki ta qara shigar da ita hakan Sam Batasan wani dogon boye boyeba.

Farko Bai wani bawa lamarin nasu mahimmanciba sbd yasan ba maganar aure akanta yanzu tasani ita kanta saita Gama karatu Amma daga baya ganin yanda ta dauki Zaid din da tsananin mahimmanci da so Mai tsanani yasa dole yashiga lamarin sbd Inayar nada raunin zuciya bazaiso soyayya ya taba masa raunintaba,rayuwarta Zata iya juyewa Takoma wata kalar daban idan raunin zuciyartata ya tabu.

Hakan yasa ya sakarwa Zaid din dama yasansa sosai yasan iyayensa Dan kuwa cikin kwanaki qalilan aka Gama binciko Masa asalinsa da iyayensa dama karatu da aiki dayakeyi anan din.

Ba laifi ya yaba da dukkanin abinda aka binciko Masa akansa daga Nan yabasa damar fara Neman inayah din
Aikuwa Dadi da farin cikinta sosai ta nunawa abbin duk da sosai yasaka Ido akansu din Dan bayason Zaid din yaqarasa hargitsa Masa tunanin 'ya dason aure Dan shigowarsa rayuwar inayah din yasa soyayyarta da aure ta qaru sosai,
Damar daya basu din yasa yanzu suke soyayyarsu hankali kwance,

Yanda take tsananin son Zaid din yasa Shima yakejin kaman zai zaune idan ba auren Inayar yayi tazama tasaba Dan kuwa bayajin zai iya rasata Bai zauceba Dan haka duka su biyun suka zaqu suyi su qarasa karatun suyi aure,

Shi yamaso ya gabatar da maganar ayi auren su kammala karatun a gidansu Amma Sam ba fuska ko damar hakan koda wasa sbd tsananin kwarjinin Abbi kesa idan yayi magana daya babu Mai kuzarin iya sake wata daban Dan haka suka barta ahakan suna soyayyarsu tunda sun samuma ya bada wannan damar.

Umma yaganah ma sosai take son ace anyiwa Inayah aure tun da qananun shekarunta zatafi morewa auren hakama A MAJEED idan ba aurarda ita yayiba yaga tafara aje Masa jikoki bazai taba tunanin yin aurenba,

Saukinsu da jin dadinsu daya dasuke godewa Allah akansa itada Inayah shine da Allah yayisa wani qaqqarfan namiji Mai siffar gaske,
Sam babu alamar manyanci ko shekaru masu yawa sosai a bayyane dashi sbd kyan jiki dakuma wani irin geamin dayake hakama tun farko haihuwace kawai ta wuri da Allah yakawo Masa bawai Dan yanada wasu shekarunba badan duniya tasan shine ya Haifa Inayah ba da bazaka dauka shine mahaifintaba,

Yanada wata irin siffar manyan matasan dasukai saurin aure da haihuwa Dan kuwa yanzu yake cikin  40s dinsa,
Idan ba kamanninsa da 'yar tasa ka kallaba zaka dauka babban 'yayanta me irin Wanda yabata tazarar Nan sosai da sosai Amma yanayin kamannin dogayen hancinsu da hasken fatarsu da Shima yafita hasken sosai yasa kallo daya zakai musu kaga yanayi irin na uba da 'ya.

Inayah dai kusan sbd mahaifinta buri da shaawar aure suka shigeta a farko sbd ji daga umma yaganah akan abbinta Aqidarsace dadaddiya bazaiyi aureba saiya aurar da ita sbd yanda abubuwa suka faru dashi acan Baya Tana qarama gurin Neman aurarrakinsa Sam shiyasa babu shaawa ko buqatan aure ataredashi saiya aurar da ita dan ayanzu babu wani ishashen dazai aibata samun 'yarsa ko kiranta da wasu sunayen Dukda yasan yanzu babu wadda zai buqata aurenta tace aa kodan tsananin dukiya da arziki da Allah ya hore Masa.

Wannan raayin na mahaifinta yasa Inayah ke qarin shaawar yin auren tasamu mahaifinta Shima yayi aure duk itama tanada burin Duk wadda abbinta zai aura saita sabu da ita ta Dan fahimtar da ita halaye da wasu raayoyan abbin datasan abbinta zai morewa auren sbd wani baudadden mutum ne da babu Mai iya gane komai game dashi idan ba itaba sai umma yaganah da itama haryanzu take cikin rashin gane kan wasu Alamuran nasa duk kuwa da uwayen shekarun data shafe dasu.

****Tsayuwa tafara yi bakin kofar shiga palonsa tayi sallama da Zaid kafin ta murda kofar tashiga bakinta daukeda sallama.

Wayarta ta saka cikin aljihun wandon kayan dake jikinta ta nufo cikin palon bayan ta rufe kofar.

Zaune yake kan _Acanva luxury velvet_ 2seater sofa sanyeda milk plain jallabiya Mai tsadan

gaske data qarasa sauyashi daga jinsin baqar fata,
Labarai yake kalla a TV hankalinsa kwance kyakkyawar fuskarsa tayi fresh tareda skin dinsa.

Takowa take a natse Tana nufar Inda yake
sanyin Aircon Gabaki daya yagama baza qamshin turarensa na _BOADICEA the victorious carbon_ koina cikin palon,

Duk yanda take kashe kudi da Bata Bata lokuta masu yawa sosai gurin gyaran fata da siyan tsadaddun designer turaruka da skin products ta rasa yanda ake matuqar abbinta na guri qamshin turarensa take Bata yake da sanyin qamshi shiyasa koyaushe cikin sauya turaruka masu tsada take Amma Abbinta koyaushe na musamman ne takasa take qamshinsa saidai kowanne nasa qamshin na musamman tsakanin ita dashi din.

Kusada dashi ta qarasa ta zauna tareda kallon kafarsa dashima take cikin qaramar half socks ta bacci
Cikin farin cikin ganinsa ta zauna Tana cewa,

"Abbi barka da dare,
Ya hanya?

Waiwayowa yayi ya kalleta cikin nutsuwa tattareda tsananin kulawarsa dake bayyanuwa a natse,

Qayataccen gajeran murmushi ya sakar mata da kusan dai haryanzu ita 'yarsa ce kawai ke samun hakan daga garesa kusan koyaushe,

Fuskarta yake kallon dan sauyin datayi ya bude Baki cikin nutsuwa yace"

Barka,
Nadawo bakya gida kinje yawon yamma right?

Look,kalla kanki,akwai sanyi atareda jikinki da alama na tabbata da yawone yasa hakan,
Umma yaganah na barinki fita Anyhow idan bananan nasani,
Kuma sbd nacinki ne,
Gashinan idonki ya nuna,
Gobe zakiga likita inshallah....

Cikin bayyanarda yar damuwa ta katsesa tana matsowa gabansa sosai tace"

Abbi na girma please kadaina cewa zanga likita,
Babu Inda naje,
Munje asibiti ne tareda Dr farhat,
Ba gashi kaga sauyi a kyakkyawar fuskanaba?

Wani kurji ne yafitomun cheek Mai zafi da damuwa sosai
Saida nayi skipping school na kwana biyu sbd hakan......

Sai alokacin yasake waiwayo da fararen idanuwansa ya zuba mata akan fuskar yana kallon gefen fuskar tata datake nuna Masa Amma fuskarsa a Dan hade jin abinda ta fada na rashin zuwa makaranta kusan kwanaki biyu

Sai alokacin ta Ankara da abinda ta fada din jin yayi shiru ya zuba mata idanuwan nasa tafara kokarin kame kame sbd idanuwan Abbinta akanta wani salon horarwane Dan kuwa tamkar hukuncine yake mata ahakan duk tayi laifi.,

Kame kamen zancen kare Kai tafara nema Amma yanayin fuskarsa yasa takasa Nemo kowacce qaryar tayi qasa da Kai cikin sanyin jiki tana jiran jin hukuncinsa akan hakan.

Dauke idonsa yayi tareda sake kame fuska Kai tsaye yace"

Ki daina zuwa all ths beauty spas da kike zuwa
Skin dinki baiyi qarfinda zai dauki wannan abubuwan ba,
Dan haka daga yau na soke zuwa kowane irin spa, beauty parlor dama komene....

Cikeda magiya ta kallesa zatai magana ya waiwayo yayi mata kallon karma naji komai daga bakinki.

Sanin Zata iya fara hawaye agurin yasa yace taje ta kwanta dare yayi.

Miqewa tayi ahankali tareda bude Baki cikin tsananin sanyi tace"

Goodnight Abbi.

Gyada mata Kai yayi yaqi kallonta Dan Sarai yasan da hawaye take yaudararsa wani lokacin yayi mata abinda takeso,

Har mamakin yake 'yar cikinsa tasan ta yaudaresa da hawaye,

Duk taurin zuciyarsa da dakewarsa tareda tsananin karantar mutane daya iya take yarasa yanda akai wani lokacin baya gane hawayen yaudararsa da Inayah keyi,

Da farko Baya ganewa sai daga Baya yafara ganewa abin yayi matuqar basa mamakin yanda tasan tayi hakan uwa uba Kuma harya yarda yahau kan hakan.

Yanzu daya gane sai Baya kallonta idanma tana kokarin farawa,

Mamakinsa daya shakkarsa daya kada taga yadaina hawa kan hawayenta ta samu wata hanyar

datafi wannan gurin kokarin biyewa dashi,

Shin tayayama tana mace Kuma qarama hartasan hakan shine takaicinsa.

Bayan fitowarta daga gurinsa bedroom din umma yaganah ta nufa saidai acan tayi hawayenta tagama umman na rarrashinta harta Gama Takoma dakinta ta kwanta ko waya Bata sake yi da Zaid ba ta kashe wayar tayi kwanciyarta.
#MAMUH#
#INAYAH#
#LOVE/ROMANCE#

_ZAFAFA BIYAR_

*_INAYAH_*
_MamuhGee_

*_GURBIN IDO_*
_Safiya Huguma_

*_SANADIN LABARINA_*
_Hafsat Rano_

*_FARHATAL QALB_*
_(Miss Xoxo)_

*_BABU SO_*
_Billyn Abdul_

_*Littafi daya 300*_
*_Littafi biyu 400_*
*_Littafi uku 500_*
*_Littafi hudu 700_*
*_Littafi biyar 1k_*

_BREAKDOWN OF ZAFAFA BIYAR VVIP SINGLE PAID BOOK_

_4 BOOKS  4500_
_3 BOOKS : 3500_
_2 BOOKS : 2500_
_1 BOOK: 1500_

YADDA ZAKU BIYA KUDIN BOOKS👇🏾👇🏾👇🏾

ZENITH BANK
HAFSAT UMAR KABIR
2270637070

SEKU TURA SHEDAR BIYA TA:
07040727902

IDAN KUMA KATI NE SEKU TURAWA👇
09134848107
[10/1, 4:10 PM] MG: *_Mamuhgee 11_*
*_Arewabooks@Mamuhgee_*
Washe gari ba wani dogon walwala ta tashi
Saima guraren 9 ta tashi Dan tun asuba tayi sallarta,

Zare dukkanin kayanta tayi ta jefa kan kujera ta wuce toilet tashige tana kokarin daura towel jikinta.

Sosai ta jima tana wankan sbd tasaba Bata lokaci gurin kyalekyalen wankan,

Sai bayan mintuna ta fito daure da milk towel kanta Kuma nade da wani towel din mara girma.

Natsatsen Qamshin shower gel dinta na AESOP Mai sanyin Dadi ne ke tashi ajikinta ta kalla Inda qaramin bedside agogonta yake ta kalli time taga goma yakusa Dan haka Kai tsaye ta nufi gaban mirror tagara shiryawa.

Moisturizer kadan ta shafa na LA PRAIRIE sai oil na Neutrogena da kome Zata shafa saita shafasa takejin skin dinta daidai.

Dama kafin ta fito daga wanka zubbi tagama gyara mata dakin ta kunna humidifier dasu fresheners masu sanyin qamshi ta fice da kayan data cire zuwa laundry.

Elira kaftan dress ta saka dark brown da scarf sai Cassandra wedge sandal ta fito gabaki daya qamshinta na JO MALONE sea salt yana gauraya iskar hanyar datake biyowa.

Kai tsaye dakin umma yaganah ta nufa tasan lokacin umman bacci takeyi sbd a qaidarta haryanzu data fara tsufa Bata daina saka hannu akan aikin abincin A MAJEED matuqar yana gari tariga ta saba
Matuqar baka ganta kitchen ba A MAJEED baya gari Dan hakan Bata komawa bacci bayan asuba saita tabbatarda abincin breakfast yagama kammaluwa a dining saita koma ta kwanta sai 12 take tashi tayi wanka ta Kuma leqawa kitchen din sakawa zubbi hannu a abincin ranar.

Kaman yanda tasani bacci umman keyi Dan hakan fitowa tayi dakin Kai tsaye ta nufi hanyar dakin cin abincinsu tana shiga abbin na shigowa ta dago ta kallesa da fararen idanuwanta

dasukaji tsadaddiyar fenty beauty mascara da eyeliner

Qamshinsa daya doke nata ta shaqa tareda dakatawa daga zaunawan da zatai cikin nutsuwa da girmamawa tareda tsananin kauna irin ta 'da da mahaifi tace"

Good morning Abbi,
Barka da fitowa.

Saida ya kalleta cikin nutsuwa ya ja kujera ahankali ya zauna yana sake kallonta ganin yanayinta na sanyi jiki har lokacin
Basarwa yayi sbd karta samu damar fara Masa hawaye agurin yace"

Morning,
Kin tashi Ify?
Ya umma yaganah?
Tana bacci ne?

Zama tayi tana cewa"

Eh Takoma bacci.

Itace ta zuba Masa breakfast din kafin tazuba nata Takoma ta zauna tafara ci.

A natse yakecin brown past din da aka hada da soyayyan dankali da hanta sbd Sarai umma yagana tasan Baya wani cin kayan fulawa sosai yafison abinci Mai suna abinci bawai wani jagwalgwalon gayuba.

Satar kallonsa Inayah keyi tanason magana akan roqonsa maganarsu ta jiyan amma tana shakkar hukunci ko dokar ta qara tsanani akan iya ta jiyan.

Kasa daurewa tayi ta aje fork din hannunta tareda dagowa ta kallesa a marairaice tace"

Abbi....

Tissue ya dauka tareda goge bakinsa kafin ya dago ya kalleta da dukkanin fararen idanuwanta ya zuba mata yana jiran abinda takeso fada.

Ganin yanda ya zuba mata idanuwansa yasata sauke Kai tana qaqalo hawaye cikin idanuwanta ta dago ta kallesa hawayen na gangarowa kan kumatunta tace"

Abbi Dan Allah kayi hkr bazan sake tsallake zuwa school ba I promise
Amma Dan Allah kada ka hanani fita ko zuwa wani gurin.

Hawayenta dake gangarowa ya kalla tareda Dan sake wani gajeran murmushi dayayi Masa zuwan bazata sbd ganin qarfi da yaji wai 'yarsa daya Rena da hannunsa keson yimasa dabara,

Duka duka Inayah nawa take?
Yaushe tayi girman da wayon datake ganin Zata iya Masa wani sisina da hawayenta tunda tasan bayaso..

Ita Bata tashi da mahaifiyaba bare ace takoya ko tagani agurinta Amma wai hartasan taringa Masa hawayen kirsa Dan yaringa barinta tana yanda takeso.

Sake fadada murmushinsa yayi kadan yana Kuma kallon hawayen nata datake tsiyaya da gaske Wanda badan yagama saninsu a yanzuba da tuni zuciyarsa zatayi 'daci da ganinsu Amma yanzu mamaki yake sosai ta yanda take iya hakan.

Numfashi ya sauke ahankali tareda zaran tissue dake kan dining din ya miqa mata yana cewa"

Ya Isa idan kingama tashi muje nine zan aje school din yau kafin na wuce office.

Share hawayen tayi da tissue din daya Bata tana jin Dadi cikin ranta na yanda kwata kwata Abbinta baya juran hawayenta.

Miqewa tayi tabiyo bayansa tareda daukan LV hanbag dinta tafito tana duba wayarta dake ringing da sunan Zaid akai.

Bata wani dauki wayarba ta jefa jaka sbd tanason samu ta lallaba abbinta yabarta taringa zuwa duk Inda ta saba zuwanta itadai tanaso gskia.

Cikin black BMW 7 series suka fita shine da kansa yake tuqa motar tana gaba zaune, gabaki daya Qamshin tsadaddun turarukansu yagama sauya numfashin motar Amma dayake motar tasace shine Wanda yafi shigarta sai nasa ya take natan sbd tuni akwai qamshinsa acikin motar.

har bakin makaranta ya ajiyeta batareda ya tankawa uban magiya ra rokon datake masaba,

Saida yayi parking ya juyo ya kalleta fuska a Dan sake cikeda kulawarsa da taushin murya yace"

Inayah.¿

Dagowa tayi ta kallesa tana kokarin qirqiro wasu hawayen dasuke son qin zuwa,
Ahankali tace"

Naam Abbi.

Wannan kukan na karya dagayau gabaki daya na sokesa Shima,
Meye amfanin hawaye Dan ki dagawa mahaifinki hankali?
Akwai wani Wanda yake Baki shawaran yin hakan ne sbd kawai kisa mahaifinki yamiki abinda kikeso?

Girgiza Mai tayi tana kallonsa da rauni tace"

No Abbi.

No Inayah fadamun gaskia sbd nasan banbawa 'yata tarbiyar hakanba,
Meye amfanin hawaye kawai sbd dagawa iyaye hankali,
Wannan ne last time dazan Kuma ganin wannan hawayen ok?

Gyada Kai tayi tareda maida hawayen dama Kuma fama taketayi akan suzo din basu zoba sbd Allah yasani batada wani dalilin kuka a rayuwarta sbd alhmdllh Allah ya wadatar da mahaifinta abinda duk take buqata a rayuwa,
Mahaifiya kawai ta rasa wadda koda ganganci ko subutar Baki Bata taba ambatar ko sunan uwa agaban abbin harma da bayansa sbd tsananin fushi da bacin ran dayake nunawa sosai wadda kusan itama sai hakan ya samu shiga zuciyarta na fushi dajin bacin rai aduk lokacinda ta tuno da dole tanada uwa kodai tabarta da mahaifinta lokacin dayake cikin zafin talaucinsa kokuma ta tafi tabarsu sbd bazata iya hakuri da wani hali daga murdaddun halayensaba Dan kuwa tasani abbin nata murdadden mutum ne itada umma yagana ne kawai suke iya Zama da abinsu sbd sunsan komai dayakeso da Wanda bayaso.

Bata saba batawa Abbinta raiba ko tayi Bata iya hakurin dacin ransa akanta Dan haka ta kallesa tareda dafa hannunsa ahankali a marairaice tace"

Abbi kayi hkr nadaina daga yau.

Gyada mata Kai yayi tareda dafa kanta cikin kulawa yace"

Shikenan kije karkiyi latti,
Ki kula.

Murmushi tasake tana cewa"

Ok bye Abbi Allah yabada sa'an aiki.

Fita motar tayi tana daga Masa hannu daya kafin ta juya ta wuce.

Neesah dake jiran isowarta taqaraso suka nufi ciki suna maganar Abbinta daya soke zuwanta spas kwata kwata.

Saida suka shige ya juya yabar gurin sai alokacin ya dauki wayarsa dake ajiye ya kunna ya nufi hanyar office.

Yau daga makaranta gida ta wuto direct basu tsaya yawon dasuka sababa na gurare
Itama Neesah yau dole gida ta wuce Amma badan sunso hakanba sai Dan bata iya take umarni Abbinta dakuma Bata Masa rai.

Kwana biyu haka suka daina yawo suka maida hankali kan karatu musamman dama sunyi nisa sosai.

Kwana biyun ita kanta umma yagana Saida taringa jinjinawa sabon umarnin na A MAJEED sbd a duniya shi kadaine yakai yakuma Isa yakeda ikon Hana Inayah yawo,

Sam batason Zama gida itada Neesah Dan hakan yanzu kwanakin duk sunbi sun wani sukurkurce sbd daga makaranta sai gida.

Shi kansa abbin yana lure da duk wani motsinsu sbd 'yarsa,
Bai taba tunanin rabata da Neesah ba sbd bincikensa tun farko dayasa ana bimasa akan Neesah batada wata gurbatacciyar tarbiya
Gata ne kawai itama da 'yanci yayi mata yawa da iyayenta suka bata Dan hakan bayan yawon shoppings dasu beauty spa sai yawon dai guraren dasuke zuwa tareda friends Amma sosai batama alaqa da harkar data shafi na banza shiyasa baiyi yunqurin rabata da 'yarsaba yabarsu suna rayuwarsu tunda dama dole Inayah zatai rayuwarta da friends.

Ahakan suka dauki tsawon lokaci har suka samu 2 weeks break a lokacinne Zaid yafara takura mata sosai akan maganar aurensu.

Kai tsaye yafito yake matsar da ita akan sosai yake buqatan aure sbd shi buqatarsa tafara zuwa na Neman mace.

Da farko fada sukayi sosai ta nuna Masa ya rabu da friends dinsa da basu dauka sex abakin komaiba sbd yanayin rayuwar turai dasuke dakuma kusan dukkaninsu tashin turai dinne.

Shawirarta ya dauka ya daina biyewasu zacks kwana biyu sbd dama sune suke tada Masa da shaawar hakan,
Da yawa yan matansu a gida suke kaisu suna wasu abubuwan gabansa gashi dama babban gidane suke zaune su ukun kowa da babban bedroom dinsa da fadeden bathroom aciki harma da closet room.

Su ukun friends ne tare suke kusan tun yarinta,

Zacks bama musulmi bane black American ne,

Sai Sufian shikuma kusanma 'dan uwansa ne sbd fmly friends ne ahalinsu.

Tare suke lafiyayyar rayuwa a gidan sbd kowannensu yanaji da kudi da gata ba laifi,
Yan mata kuwa kusan kullum cikin sauyawa sukeyi babu ranarda mace Bata kwana gidan
Idan zacks Bai kawoba Sufian zai kawo Dan hakan yau da gobe suka ringa saka Zaid cikin
yanayi na damuwa gashi yanzu tsakani da Allah yakan ji shaawar mace lokuta da dama.
Kwana biyu yafara kasa daurewa shine yafara takurawa Inayah maganar aurensu.

Yauma kusan fadan sukayi akan maganar cikin yanayi na takaicinsu zacks tace Masa"

Baby nafada maka Abbi bama zai kalleniba naje da maganar Kuma shikenan nice zanje na
rokesa akan ayi aure yanzu?
Kana tunani kuwa?
Please ba Abbi ba Nima banajin na shiryawa auren yanzu idan har sbd wannan maganar
kakeson auren yanzu...bazan iyaba please baby mubar maganar Nan banason jinta tana
damuna ma.

Shima ransa Dan baci yayi Dan haka Bai Kuma tayar mata da maganarba saiya koma kiran dad
dinsa yana matsa Masa sosai akan maganar auren Dan hakan dole dad din nasa ya nema A
MAJEED da maganar idan da hali suna son ayi auren yanzu.
##MAMUH#
#INAYAH#
#RIBA BIYU#
#LOVE/ROMANCE#

_ZAFAFA BIYAR_

*_INAYAH_*
_MamuhGee_

*_GURBIN IDO_*
_Safiya Huguma_

*_SANADIN LABARINA_*
_Hafsat Rano_

*_FARHATAL QALB_*
_(Miss Xoxo)_

*_BABU SO_*
_Billyn Abdul_

_*Littafi daya 300*_
*_Littafi biyu 400_*
*_Littafi uku 500_*
*_Littafi hudu 700_*
*_Littafi biyar 1k_*

_BREAKDOWN OF ZAFAFA BIYAR VVIP SINGLE PAID BOOK_

_4 BOOKS  4500_
_3 BOOKS : 3500_
_2 BOOKS : 2500_
_1 BOOK: 1500_

YADDA ZAKU BIYA KUDIN BOOKS👇🏾👇🏾👇🏾

ZENITH BANK
HAFSAT UMAR KABIR
2270637070

SEKU TURA SHEDAR BIYA TA:
07040727902

IDAN KUMA KATI NE SEKU TURAWA👇
09134848107
[10/3, 11:07 AM] MG: *_Mamuhgee 12_*
*_Arewabooks@Mamuhgee_*
Dad din zaid yasan Sarai waye A MAJEED Dan hakan Bai tsaya nemansa a wayaba sbd sanin babu abinda zai gane a wayar tunda A MAJEED din ba wai son auren yanzu yakeba yakuma sanar dasu hakan batareda ya fada dalilinsaba saidai Kuma kusan duk Wanda yasansa yasan dalilin nasa ba boyayye bane duba da yanda yake Da zurfi da ilimin boko sosai daya Gama ratsasa sunsan babu yanda mutum irinsa zai aurar da yarsa qwalli daya dazata gadi tarin dukiya da companies dinsa batareda tasamu ilimin itama Mai zurfiba  Amma ya suka iya tunda sunaso dole haka ya tattara ya tsaro tafiya ya taso zuwa qasar.

Shi dad din tun farko bakin rai bakin fama yakeson auren tsakanin 'yayan nasu sbd burinsa nason qulla alaqa Mai qarfi da A MAJEED,

Babu wani Mai son abun duniya da kudi daba zaiso shi ko 'dansa su auri 'yar A MAJEED qwaya daya tal ba wadda zai iya bada duk tarin himilin dukiyarsa akantaba
Dan haka ba dauki bare wasa shi kam so yake ayi auren kota yaya Dan Inayah idan tana hannun 'dansu tamkar suna riqene da mukullin dukiyar A MAJEED da Baya tabuwa bare juyiwa ga kowa,Dan banzan naira da dollar sungama zauna Masa tako Ina,sun girmesa Sbd har

lokacin baiyi shekarunsuba badan yanada zuqeqiyar budurwar 'yaba ai yanada sauran lokaci a cikin matasa Amma dai koma menene yaro da kudi abokin manya dama abokanan huldarsa manyan ne na gaske.

Zuwan dadyn Zaid Sydney yasa damuwar da Inayah tafara shiga ya dan fara raguwa sbd gabaki daya kwata kwata yanzu itada Zaid din kullum cikin hayaniya suke,

Bazata iya daukan fada bare rabuwa da Zaid ba
Ayanzu din tafison Dad din nasa yayiwa abbin mgn idan ya amince ayi auren Dan gskia tana tsananin son Zaid dinta koma menene ayi auren zatai maganin wannan iskancin da yayi mata daga baya.

Yau daga makaranta Saida su biya ta siyo wasu abubuwan wankanta dasu undies da Bata rabo da siya akai akai,

Sai yamma suka dawo Shima tun acan take waya da abbin akai akai tanaji idan yadawo gida sbd kada ya rigasu komawa yaga sunyi yammacin dawowa.

Da motan Neesah suka dawo sbd yauma Abbinta ne ya ajeta makarantar Dan dama haryanzu data girma dinnan idan yana gari yawanci shine yake ajeta school saidai driver yaje ya daukota kokuma su dawo a motar Neesah.

Neesah Bata shigoba ta wuce Dan hakan itama Kai tsaye tana shigowa bakowa a palo dakinta ta nufa.

Ajiye kayan hannunta tayi tana ajiye numfashin 'yar gajiya da yunwa datake ji Dan haka tubewa tahi ta fada toilet tayo wanka tafito ta sanya Abayar sallarta tana idarwa tayi adhkar ta miqe ta sanya ash riga da wandon Burberry masu kauri saidai qananun size ne Dan sun zauna daidai jikinta,basu matsetaba hakama basuyi mata yawaba daidai jikinta.

Sponge resort Slippers ta zuro ta fito tana qamshinta hankali kwance.

Dakin umma yagana take kokarin zuwa saiga umman ta fito.

Cikin shagwabe fuska ta rungumo hannun umman suna juyawa zuwa dakin cin abinci tana cewa"

Umma yaganah yunwa nakeji sosai.

Murmushi umman tayi tareda Dan janye jikinta daga Inayar tana cewa"

Haryanzu kin kasa iya fara gaisuwa kafin komai ko Inayah?

Sake kwantar da kanta tayi kafadar umman tana cewa"

Umma yaganah kullum fa Ina gaisheki kafin nafita idan nadawoma inayi ranarda na manta ba sai ayi hakuri Amin uzuriba for God sake,Kuma ma fa na........

Qamshin Turaren Abbinta yasata shanye abinda Zata fada din suka kalla hanyar palonsa atareda umma yaganah aikuwa shi dinne tafe cikin nutsuwa da kwanciyar hankali.

Sanye yake da fararen Adidas riga da wando masu kauri hular dake hadeda rigar itace rufe akansa
Qafafunsa kuma black santoni slippers ne.

Gabaki daya Abbinta idan yayi shiga tamkar matashi yake komawa musamman irin wainnan shigar da yakeyi idan zaiyi geamin(exercise/motsa jiki) ko idan zai kwanta ranarda yakejin sanyi kenan,

Yawan geamin dinsa yasa kullum yake sake Zama tamkar wani sabon matashin da yanzune yake lokacinsa sudaima sun rasa gane irin kyan jiki da kyan siffarsa daya hanasa manyanta sosai.

Umma yaganah ce tafara bude Baki tana kallonsa tace"

ABDULMAJEED barka da fitowa.

Cikin yar girmamawa ya Dan kalleta kadan tareda dauke idonsa akanta yana cewa"

Mun wuni Ify umma yaganah?

Wata jarabawa kokuma ace lalura datake kansa tsawon shekaru shine Baya kallon mata kallon daya wuce daya zuwa biyu,

Sam ya dade da rufe shafin mace ata kowanne fani na rayuwarsa bayan 'yarsa,
Duk huldar aiki dazata hadasa da mata Baya wani maida hankali sosai akansu Wanda Kuma kusan ba kowane ya fahimci hakanba tunda dama shi ba mutum ne Mai sakewa mutuneba shiyasa baa wani ganewa
saidai umma yaganah da Inayah dasuka Sansa ciki da Bai sune sukasan babu macen dayakewa kallon daya wuce biyu zuwa uku,

Umman ma haryanzu idan yayi mata kallo daya zuwa biyu koda suna magana ne Baya qarawa shiyasa da yawa idan kana Masa bayani saika dauka hankalinsa Baya kanka and yafi maida hankali kan wani abun daban ko waya haka Amma Kuma ahakan yafi fahimtar bayanin da ake masa.

Wainda suka 'dan Sansa da kadan daga halayensa idan suna magana dashi sukaga Baya wani abun daban ya tsaya yana saurarensu to kuwa sun San tabbas Bayada niyar saurarensu ne,idan kanason Kama mutuncin kanka saika dakata kabar maganar Dan ba lokacinta zaiyiba.

Zama sukayi dukkaninsu a dining Inayah ta zubawa kowa abincin kafin Takoma ta zauna itama bayan ta zuba nata,

White rice ce da chicken vegetables with scrambled eggs.

Suna fara cin abincin Inayah ta kalli abbin dayakecin abincin a natse kunnuwansa na sauraren sautin yanayin cin abincinta take ya fahimci akwai maganar datakeson yi.

"Abbi" ta furta sunan ahankali cikin kulawa da bayyanarda 'yar shagwaban data taso acikinta.

Kallonta umma yaganah tayi cikin kulawa ya katseta da cewa"

Ba yanzu ba Inayah,
Bakiga Abbinki yanacin abinciba?
Surutu lokacin cin abinci baida amfanin kinmatane?

Marairaice fuska tayi cikin son fadar abinda yaketa nuqurqusanta Kuma tasan Idan ba fada Masa tayiba Dad din Zaid yayi Masa zuwan Kai tsaye da bazata ransa zai baci akan da sanin ta akazo maganar,

Bazata iya daukan fushi ko bacin ran abbintaba akanta Dan haka Kai tsaye takuma kallonsa bayan tayiwa umma yaganah fuskar riqon tabarta tayi magana.

Abbi Dad din Zaid Yana gari yazo fa....

Ahankali ya qarasa hadiye sauran abincin dayake bakinsa ya dauki ruwa mara sanyi sosai dake gabansa cikin glass cup yasha ya ajiye sauran ya dauki tissue Saida ya goge bakinsa ya dago da manyan idanuwansa ya kalleta hankali kwance yace"

Yes,Uhum?
Dad din Zaid Yana gari zan Masa wani Abun ne?
Gurina yazo ne?

Abbi dama gurinka ne zaizo kuyi magana,karyazo ne baka saniba ranka ya baci Abbi shine nafada maka Kuma banice nace suzoba Abb...

Umma yaganah ya kalla Kai tsaye da tambayar

"Kinsan da hakan ne umma yaganah?

Ta sanar dake Zata basu Daman zuwa neman aurenta?

Ajiyar zuciya umman ta sauke cikin sanyin jiki sbd Inayah dai Bata gane kwaba,

Kallonsa take cikin sanyin jiki tace"

Ta sanarmun da mahaifin nasa zaizo Amma na kaina na Kira Zaid din nace su dakatar da zuwan sbd Jan magana daya koyaushe baida amfani tunda dai anbasu auren Inayar
Yin auren ne dai tunda anfada musu ba yanzuba na rasa naci irin na 'yaran yanzu tunda ba cewa akai a gaban zaa fasaba...

Jin shirunsa Yana saurarensu yasa dukkaninsu suka Sha jikinsu sbd sanin hakan abinda yake nufi,

Dukkaninsu sun fahimci bacin ransa akan hakan shiyasa suka sake yin wani tsamo tsamo.

Cikowa idanuwan Inayah sukai da hawaye batareda ta saniba cikin sanyin murya da sigar ban hakuri ta taso tadawo gefensa tareda Dafa hannunsa ahankali tana cewa"

Abbi Banice nace suzoba wlh,
Nayiwa Zaid din maganar kada dad din yazo Amma baijiba,
Abbi wlh bani bace...

Batareda ya kalletaba yace

"It's okay saiyaxo Ina jiransa.

Miqewa yayi tareda kallon umma kadan yace"

Mu kwana Ify umma yaganah.

Allah ya tashemu Ify" tafada itama tana bin bayansa da kallo ranta babu Dadi da yanayin,

Babbar matsalar basa wani gane bacin rai ko fushinsa bare kasan halinda kake ciki shiyasa koyaushe irin wannan kuskuren yafaru sun ringa Kara kaina kenan gurin samun sanin yanda ransa ya dauki Al'amari.

Bayan barinsa gurin Kallon umma yaganah Inayah tayi da raunannun idanuwanta zatai magana umma ta tareta da cewa"

Inayah meyasa kikai maganar Nan?
Maimakon ki dakatar dasu Zaid din shine Zaki Kuma kawo maganar gaban mahaifinki bayan kinsan bayason maimaicin zance,

Anyita maimaita zancen Nan Kuma kinfi kowa sanin mahaifinki magana daya yakeyi akanki meyasa bazakiyi respecting hakanba?

Yanzu gashinan zakiwa kanki Dan kuwa Abbin zai iya Hana auren gabaki daya yace su hakura suje su nema wata su aura idan sunaga bazasu iya jiranba
Kinga kuwa wa garin ya waya.

Batada abin fada sbd jikinta daya Gama mutuwa da yanayin mahaifinta daya qi barin su gane yanda ya karbi zancen.

Cikin sanyi ta dauki orange juice din dake gabanta ta Sha sosai ta aje cup din sbd bazata iya cin abincinba Kuma.

Miqewa tayi tareda yiwa umma yaganah Saida safe ta wuce dakinta itama.

Itama umman kammalawa tayi ta miqe tabar dakin ta dauki sauran abincin datasan zai moru takai fridge ta jera kafin ta wuce nata dakin zubbi tazo ta tattara gurin ta gyare Takoma dakinta itama.

Bayan isarta daki ta Gama duk abinda zatayi ta hau makeken gadonta ta kwanta tareda daukan wayarta ta saka Kiran Zaid.

Daukan wayar yayi tun kafin yayi wata magana tace"

Zaid please ka dakatar da zuwan dad gurin Abbi banason cigaba da Bata ransa akan maganar wani auren yanzu,
Nidai gskia mu haqura abari sai lokacinda Abbina yace koma yaushe ne zamu jira
I don't want to stress him with unnecessary abubuwa kaman hakan tunda yace ajira kawai ajira Dad dinka yakoma please...

Inayah are you out of your mind or what?"" yafada cikin Dan daga murya.

Kinajin kanki da abinda kike fada kuwa?
Dad ya taso all the fuckin way from Nigeria yazo kice yakoma sbd kada a dama Abbinki?
Are you for real?Kinajin kanki kuwa?

Zaid please karmu batawa juna Rai abanza mubar maganar auren Nan yanzu sai gaba....

Datse wayar yayi ya kashe gabaki daya ya jefar gefensa Dan zuciyarsa tafara baci sosai da yanda koyaushe Abbinta shine gaba shine yafi kowa mutunci,yanaji kaman mahaifinsa take kokarin ciwo mutunci Dan haka cigaba da wayarsu yanzu zai iya hadasu fada sosai shiyasa ya kashe din.

Inayah ma wayar tabi da kallo cikeda mamaki da Dan takaici,
Ita Zaid yake kashewa waya yau?
Wai kodai bayan matsalarsa ta buqatan aure yanada wata matsalar ne da ita Bata saniba Dan kuwa wlh bazata dauka wannan wulaqancin tun yanzuba tana magana ya kashe mata waya.
##MAMUH#
#A MAJEED
#INAYAH

_ZAFAFA BIYAR_

*_INAYAH_*
_MamuhGee_

*_GURBIN IDO_*
_Safiya Huguma_

*_SANADIN LABARINA_*
_Hafsat Rano_

*_FARHATAL QALB_*
_(Miss Xoxo)_

*_BABU SO_*
_Billyn Abdul_

_*Littafi daya 300*_
*_Littafi biyu 400_*
*_Littafi uku 500_*
*_Littafi hudu 700_*
*_Littafi biyar 1k_*

_BREAKDOWN OF ZAFAFA BIYAR VVIP SINGLE PAID BOOK_

_4 BOOKS  4500_
_3 BOOKS : 3500_
_2 BOOKS : 2500_
_1 BOOK: 1500_

YADDA ZAKU BIYA KUDIN BOOKS👇🏾👇🏾👇🏾

ZENITH BANK

HAFSAT UMAR KABIR
2270637070

SEKU TURA SHEDAR BIYA TA:
07040727902

IDAN KUMA KATI NE SEKU TURAWA👇
09134848107
[10/5, 8:23 AM] MG: *_Mamuhgee 13_*
*_Arewabooks@Mamuhgee_*
Da 'dacin Rai duka suka kwana a daren ,
Inayah Kuma harda matsuwa tayi garin ya waye ta nemesa taji dalilinsa na kashe mata waya sbd ko Abbinta baya kashe mata waya shi dayafi kowane namiji daraja agurinta da rayuwarta.

Duk yanda Abbi yakai ga bacin rai baya taba Bari agane Dan haka da safen koda ya fito kyakkyawar  fuskarsa na ayanda take koyaushe ba damuwa.

Black Armani's ne ajikinsa sosai yayi fresh acikin black kala din,

Cikin sanyi ta kallesa tanason shagwabe Masa Amma tunanin Tayi Masa laifi daren na jiya yasa ta Dan nutsu duk da hakan cikin marairaicewa tace"

Good morning Abbi" tana qarasowa gurinsa itama shirye cikin milk sleeves riga da skirt na Balenciaga.

Morning Inayah" ya amsa Yana kallon yanda idanuwanta sukai zuru zuru sbd daren jiyan da Bata samu bacciba.

Dining suka zauna bayan ya gaisa da umma yaganah yasake kallon Inayah din da itama taketa qara wani kalar tausayi ganin take ya nuna ya lura da yanayinta na rashin baccin da Bata samuba Kuma tasan dole zai nuna damuwarsa akan hakan shiyasa take sake yin kalar tausayi.

Black tea Ginger tea Mai zafi aka fara zuba Masa ya dauka yafara Sha ahankali tareda Dan sake kallon fuskar Inayah din ya dauke fuska Kai tsaye ya bude Baki cikin nutsuwa yace"

Inayah¿

A marairaice tace"

Yes Abbi¿

Kallonta yayi bayan ya aje cup din hannunsa fuska a Dan matse yace"

Next abinda zakiyi na soke alaqarki da kowanne namiji sai bayan kin Gama karatu kwata kwata shine kici gaba da saka damuwar soyayya aranki harya hanaki bacci irin haka,

Umma yaganah ya kalla cikin jaddada zancensa yace"

Yaushe tasan wani soyayya hakane?
Ki ringa Mata fada sosai idan ba hakanba zan tattara mubar qasar gabaki daya mu koma Nigeria ko Zata maida hankali a karatun can.

Hawaye takeson yi Amma tunowa da ya Hana yasata maida hawayen cikin sanyi tace"

Abbi Dan Allah kayi hkr,
Ba tunanin komaine yasa banyi bacciba inada test ne yau so I had to study all night...

Waiwayowa yai ya watsa Mata manyan idanuwansa ahankali Yana sake mamaki da jinjinawa sauyin sabbin halayenda Inayah ke dauka,
Yaushe Kuma ta iya harda yimasa qarya?

Sauke Kai tayi qasa tana Dan sosa wuyanta gabanta na faduwar kada yagane qaryarta saidai Batasan ta makaroba.

Qarasa Shan tea dinsa yayi Bai wani Abinci sosai ba ya kammala ya miqe Yana cewa"

Muje zan ajeki school.

Satar kallon umma yaganah tayi tana neman qaryar dazata Kuma shimfidawa yatafi yabarta ta tafi school din da kanta Dan dole tana buqatan biyawa gurin Zaid suyi magana.

Rasa abin fada tayi dole badan tasoba ta miqe suka bar gurin umma nai musu adduar dawowa lfy.

Shi kadaine ya amsa Banda ita data shiga tunanin abinyi Dan yanzu tasan kila Abbin zai qara Mata tsananin fita akan na dah.

Yau bashine yake tuqa motarba driver dinsa ne yake jansu.

Har suka Isa makarantar kame kamen basa hakuri takeyi Amma Bai wani bi takan zancen nataba saima zancen karatun dayayi Mata daban.

Suna Isa aka sauketa suka wuce sai alokacin yabi bayanta da kallo,
yanajin tausayin 'yarsa fiyeda komai,

Hakama Baya iya hakurin damuwarta,

Ya rasa waye yake gurbata Masa tunani da tarbiyar 'ya akan ire iren hakan,

Kwata kwata haryanzu bayajin sha'awar kowace irin mace bare marmarin ajiyeta shiyasa yake tsananin mamakin yanda Inayah ta qwallafa Rai a soyayya da son aure tunda ba ganin tayiba a gidansu ana soyayyar, hasalima shi soyayyarce sam baisan yama akeyintaba bare harka Gama macewa akan wani kaje kana Hana kanka bacci a wofi.

Motar Abbin na barin makarantar ta fito zuwa coffee shop din dake makarantar ta samu Neesah dake can ta zauna tareda fidda wayarta batareda ta iya wata doguwar maganar da Neesarba tafara saka Kiran zaid.

Kasa samunsa tayi dole qarshe tabar Masa sakon murya da cewa idan ya kunna waya yakirata Kuma ya tabbata Dad baije gurin Abbinta ba sbd zasu iya yiwa kansa Abbin ya dakatar da soyayyarsu sai gaba din.

Bayan Gama tura Masa sakon muryan aje wayar tayi gabanta zuciyarta ba wani Dadi ta Dan yamutsa fuska tareda Kiran sunan waiter a tushe tace"

2 Cappuccino's please.

Kallonta Neesah tayi tana cewa"

Kodai zamu samesa ne?

Bazai tsaya sauraren wannan ba namafi zatan Dad din nasa ya riga Abbi Isa office dinsa jiransa.

Kasa cewa komai tayi Saida aka kawo Mata cappuccino din ta fara Sha ahankali kafin tace"

Banajin komai sai bacin ran mahaifina,
Zuwan dadyn Zaid zai fusata Abbi Kuma na fadawa Zaid kada yaje Amma Yana banza da zancen yakuma Dan akan Abbina bana daukan wannan so gwarama ya daina wannan saurin.

Bari naji Inda yake saimu samesa" cewar Neesah tana fidda wayarta daga qaramar Louis Vuitton handbag dinta.

Kinason Abbi ya daina kulani kwata kwata yayi fushi danine?
Kinsan halinda mahaifina zai shiga kuwa idan yaji naje gidan namiji
Gskia bazan iyaba,
Bari anjima idan Bai kiraba na sake kiransa.

Maida wayar Neesah tayi tana cewa"

Amma dai bafa lallai yazoba Sai sungama magana da Abbin hakan Kuma shine qarshen Bata komai.

A qasan maqoshi ta furta"

